# CIN GABA DA AIKI TARE

# KOS NA 103

## YIN GIRMA A CIKIN KRISTI



Na ɓoye maganarka a cikin zuciyata domin kada in yi maka zunubi.

Zabura 119:11

www.ProgressingTogether.com
info@progressingtogether.com
FEBURAIRU 2021

# KOS NA 103 –Yin Girma a cikin Kristi

## *Manufofin Kos na 103*

1) *Domin a gane tushen horarwar Krista wanda Allah yake amfani da shi domin taimako mu san shi da kyau da kuma yi rayuwa a cikin hanyar faranta masa rai.*
2) *Domin inganta ƙara yunwar yin kurkusa da Allah ta wurin amfani da waɗannan kayan ruhaniya a cikin rayuwarmu.*
3) *Domin kafa halaya na amfani da waɗannan horarwa na ruhaniya kullum.*
4) *Domin girma cikin godiya na yadda Allah yake amfani da waɗannan horarwa domin yǎ canza mu yǎ kuma ƙarfafa sauran su neme su.*

## *Darusa*

| | |
|---|---|
| ❶ | Ruhu-Mai Taimakonmu |
| ❷ | Kalma-Abincinmu |
| ❸ | Addu'a-Magana da Uba |
| ❹ | Azumi da Nazari-Matsowa Kurkusa da Uba |
| ❺ | Ikkilisiya-Sabuwar Iyalinmu |

## *Gabatarwa*

Ko kana marmarin yin kusa da Allah? Kana so ka yi tafiya a cikin babban biyayya ga kalmarsa? Ko kana marmarin sauran Krista su zo kewaye da kai su ƙarfafa ka? Kana so ka cika da farin cikin Ubangiji ka kuma ɗanɗana salamarsa? Idan amsar "I" ne, ga kowane daga cikin waɗannan tambayoyi, to, ke nan wannan kos saboda kai ne.

A cikin wannan kos, za mu duba kayan da Allah ya ba mu domin su jawo mu kurkusa da shi. Za mu koya yadda za mu yi tafiya cikin babban biyayya ga kalmarsa domin mu ɗanɗana ƙauna da ƙarfafawar Ikkilisiya. A cikin darasi 1, za mu ga Allah bai bar mu kaɗai ba amma ya aiko Ruhunsa Mai Tsarki domin yǎ ba mu ƙarfi, da jagora, da kuma ya yi mana ta'aziya. A cikin darasi 2, za mu ga yadda za mu bincike Kalmar Allah mu sa cikin aiki a rayuwarmu.  A cikin darasi 3, za mu sami ƙarfafawa domin inganta dangantaka tare da Uba ta wurin addu'a. A cikin darasi 4, za mu ƙara inganta wannan ta wurin duba azumi da nazarin Kalmar Allah. A ƙarshe, a cikin darasi 5, za mu ga muhimmancin miƙa kai cikin ƙwazo a cikin Ikkilisiya da yadda za ka haɗa kai da sauran masu bi a cikin cuɗanyar ƙarfafawar da zai taimake mu domin mu yi kurkusa da Allah.

Cikin dukan wannan kos, za ka koya game da kayan da Allah cikin alherinsa yake tanada mana domin yǎ jawo mu kurkusa da shi. Za ka sami kalubalai wadda za isa ka fara amfani da waɗannan kaya a cikin rayuwarka ta kullum. **Karin bayyani** a ƙarshe na wannan kos zai tanada hanyoyi na aikatawa domin kafa sabon hallaye bisa kowane darasi.

## *Labari*

Shugaban kungiyar ku zai sa ku kallo ko sauraron sheda mai alaka da batun wannan Darasi

# Darasi ➊: Ruhu – Mai Taimakonmu

## Yohanna 14 – 16

Suna: ________________________________________ Kwanan wata: _____________________

## *Manufofin Darasi*

1. *Domin a gane nawayar Ruhu Mai Tsarki cikin taimaka wa mai bi yă yi rayuwar biyayya da rayuwar Krista mai nasara.*
2. *Domin a ɗanɗana canjin rayuwa ta dalilin rayuwar kullum a cikin ikon Ruhu Mai Tsarki.*
3. *Domin a gane aikin Ruhu Mai Tsarki a cikin duniya marar gaskata.*

✧

Ba za ka taɓa zama kai kaɗai ba. Allah koyaushe yana tare da kai. Wane irin girma da mamakin alkawari ke nan! Kafin Yesu ya tashi zuwa sama, ya yi alkawari cewa zai aiko da wani 'Mataimaki' yă kasance da almajiransa har abada. Wannan 'Mataimaki' shi ne Ruhu Mai Tsarki. Ko kana karanta Kalmar Allah, da addu'a, da wa'azi, ko yin ƙoƙarin yin abin da yake daidai, Ruhu Mai Tsarki yana tare da kai domin yă taimaka, yă ƙarfafa, yă yi jagora yă kuma taimake ka. A cikin wannan darasi za mu yi nazarin shafofi biyu daga sura 14 – 16 a cikin Bisharar Yohanna domin mu gane wanene Ruhu Mai Tsarki, nawayarsa a cikin rayuwar mai bi, da yadda yake cuɗanya da duniya marar gaskata.

**Karanta Yohanna 14:15-17 a hankali.**

### ① Alkawarin Yesu na wani 'Mataimaki'.

Idan kana ƙaunar Yesu (14:15), Menene ya ce za ka yi?

_______________________________________________

Menene Yesu ya yi alkawari ga waɗanda suke ƙaunarsa kuma suna kiyaye umarnansa (14:16)?

_______________________________________________

Kalmar nan da Helenanci wanda aka yi amfani domin 'Mataimaki' a nan ita ce 'Parakletos'. Ana kuma iya juya ta zuwa Mashawarci, Mai ta'aziya, ko Masaƙaici. Ma'anar wannan kalma ita ce wanin da yake tafiya tare domin taimako. Yesu yana tafiya kuma yana so yă ta'azantar da almajiransa a cikin baƙin cikinsu na bankwana. Ya kuma so yă tabbatar musu za su sami mai jagora da taimako nan gaba.

## ② Wanene Ruhu Mai Tsarki?

A cikin Yohanna 14:17-26, Yesu ya bayyana muhimman halaya sau da yawa na ‘Mataimaki’ domin almajiransa. Haɗa fi’ilin Nassi da kalmomin da suna bayyanin Ruhu Mai Tsarki. Waɗansu fi’ilin za a haɗa su fiye da kalma ɗaya. Amsa bisa tsari ya tanada domin fi’ili na biyu.

| Kalmar Kwatanci | Shafofin Nassi | Amsoshi |
|---|---|---|
| A. Marar ganuwa<br>B. Ruhu, ba jiki ba<br>C. Madawwami<br>D. Cikakkiyar Gaskiya<br>E. Yana ko’ina<br>F. Mai sanin duka | Zai kasance tare da almajirai har abada. (14:16)<br>Shi ne Ruhun Gaskiya. (14:17)<br>Duniya ba za ta gan shi ba. (14:17)<br>Yana zama tare da kai kuma zai kasance a cikinka<br>Yana koyar maka dukan kome. (14:26) | <br>B, D |

Waɗannan halaya, da aka bayar menene za ka kamala game da Ruhu Mai Tsarki?

---

## ③ Irin aikin Ruhu Mai Tsarki a cikin rayuwar almajiran Yesu.

Ruhu Mai Tsarki yana ba masu bi iya rayuwar cike farin ciki da rayuwar biyayya.

**Sāke karanta Yohanna 14:15-17.** Ruhu Mai Tsarki zai taba rabu da almajirai?

---

Yaya kasancewar Yesu ya ƙarfafa almajirai?

---

Yaya kasancewar Ruhu Mai Tsarki zai ƙarfafa yă kuma yi musu ta’aziya?

---

**Sāke karanta Yohanna 14:23.** Yesu ya ƙara cewa, “Duk wanda yana ƙaunata, zai kiyaye kalmata.” ‘‘Su wanene za su mai da almajirai gidansu in sun yi wannan’’?

---

Wannan ayya ta na taimaka mana domin mu gane uku cikin ɗaya na Allah (Uba, da Ɗa, da Ruhu Mai Tsarki) a cikin Trinity. Ba wai Ruhu Mai Tsarki ne kaɗai yake zama a cikin almajiri ba, amma ta wurin Ruhun, duka Allah Uba da Yesu suna zama a cikinsa. Idan Ruhu Mai Tsarki yana zama a cikin ka, sa’an nan dukan cikakken Trinity suna zama a cikinka domin taimako da kuma karƙafa ka.

**Sāke karanta Yohanna 14:25-26**. Wane irin aiki ne kuma da Ruhu Mai Tsarki yake yi a cikin rayuwar almajiri?

**Karanta Yohanna 15:18 – 16:15 a hankali.**

## ④ Aikin Ruhu Mai Tsarki a cikin duniya marar gaskatawa.

Sa'ad da Yohanna ya yi amfani da kalma 'duniya' a cikin wannan shafi yana nufi ga dukan waɗanda suka ƙi Allah kuma hanyoyinsu sun ƙirƙiro haka. Suna gāba da Yesi da masi binsa.

Wane irin hali ne duniya take da shi ga masu bin Yesu? (15:18-21)

---

Don me duniya tana yin irin wannan hali?

---

A cikin wannan ganewa, menene Yesu ya faɗa Ruhu Mai Tsarki zai taimaki almajirai su yi (15:26-27)?

---

Don me Yesu ya faɗa wa almajiransa cewa 'zai kasance da riba a gare ku in na tafi' (16:7)?

---

Menene aikin Ruhu Mai Tsarki a cikin rayuwar waɗanda ba su san Allah da kuma suna rayuwa bisa tsarin duniya? (16:8-11)

---

Ba aikin ne ka shawo kan marar ba da gaskiya. Allah ya kira ka domin ka zama mai shaidarsa ne. Aikin Ruhu Mai Tsarki ne ya kāshe mutum yǎ kuma kawo su ga tuba. Kada ka kasance da rashen ƙarfi idan ka shaidar da ka yi bai canja zuciyar wani nan da nan ba. Ci gaba da addu'a domin su ka kuma roƙi Ruhu Mai Tsarki ya kāshe su yǎ kuma kawo su ga tuba a cikin rayuwarsu.

## Ayyukan ra'ayi

1. Rera daya daga cikin wakokin sujada (ko wata waƙar ra'ayinka). Sa'an nan ka ɗauki lokaci cikin yabo, da godiyar Allah domin kyautar Ruhu Mai Tsarki wanda yana rayuwa a cikinmu har abada.
   – Holy Spirit, living breath of God (Ruhu Mai Tsarki, rayayyen numfashin Allah)
   – Spirit of the living God (Ruhun rayayyen Allah)
   – Hymn of the Holy Spirit (Waƙoƙin Ruhu Mai Tsarki)
2. Kalla wannan finafine 'What does it mean to be filled with the Holy Spirit?' ('Menene wannan yana nufi mutum yă cika da Ruhu Mai Tsarki?'). Sa'an nan, yi addu'a a kan ya kamata ka ci gaba da cikawa da Ruhu Mai Tsarki.

## Aikatawa (Sa cikin aiki): Yaya za mu zurfafa dangantakarmu da Allah ta wurin Ruhu Mai Tsarki?

1. Lura da abin da muka koya a cikin wannan darasi. Yaya kasancewar Ruhu Mai Tsarki yana ƙarfafaka yau? Tattauna wannan a zaman ƙungiya.
2. A zaman masu bi, ya kamata dukanmu mu nemi zaman ci gaba da cikawa da Ruhun Mai Tsarki na Allah. Ga waɗansu matakai masu sauƙi waɗanda za su zama mana da taimako mu yi wannan:
   – Zo cikin ƙasƙanc a gaban Allah cikin addu'a
   – Furta wani zunubin da ka sani
   – Miƙa kanka ga yin nufin Ubangiji
   – Roƙe shi yă cika ka da Ruhunsa
   – Yabe shi ka kuma gode masa domin kasancewarsa da dukan kyautai nasa masu kyau
   – Yi rayuwa ciki farin ciki, da biyayya da bangaskiya
3. A zaman ƙungiya, ku karanta A.M. 4:23-31 kayi addu'a cewa ikon Ruhu Mai Tsarki zai cika kowanenku a wannan mako. Ku yi shirin ba da shaida mako mai zuwa game da tafiya a cikin Ruhu.
4. Kafa lokacin sujada da bincike kowace rana a wannan mako. Domin ra'ayin karanta Littafi Mai Tsarki kowace rana a kan hidimar Ruhu Mai Tsarki a cikin rayuwarka, dubi **ƙarin bayyani G** a ƙarshen wannan kos.

## Faɗa

Wannan mako, faɗa wa waɗansu abin da ka koya a cikin wannan darasi. Za ka iya maimaita darasin da wani.

# Darasi ❷: Kalma-Abincinmu

## Zabura 119

Suna: ________________________________________ Kwanan wata: ______________________

## *Manufofin Darasi*

1. *Domin a gane muhimmancin irin aikin kalmar Allah a cikin rayuwarmu na masu bi.*
2. *Domin a koya yadda mutum zai bincike Littafi Mai Tsarki mara wuya.*
3. *Domin mutum yǎ saba da binciken kalmar Allah a kowace rana daidai lokaci.*
4. *Domin a iya faɗa yadda biyayya da kalmar Allah tana kawo albarku da tsarewa cikin rayuwar mai bi.*

✧

### Yaya kake ci gaba a kan

1. Menene muhimman kalmomin darasi na ƙarshe?
2. Menene ya faru lokacin da ka faɗa wa waɗansu abin da ka koya?
3. Menene ya canza a cikin rayuwarku ta dalilin waɗannan koyarwa?

### Karanta 2 Timoti 3:16-17 da Zabura 119:105.

Yayin da muka gani a cikin darasi na farko, Ruhu Mai Tsarki shi ne jagoranmu da mashawarcinmu a duniya. Shi yana taimkon masu bi su gane su kuma tuna Kalmar da Allah ya bayyana, wato Littafi Mai Tsarki. Littafi Mai Tsarki ba wai wani takarda kawai ba, ainihinta 'numfashi ne daga wurin Allah' kuma ru'uyar Allah ne mai iko, mai bayana yadda yake, da yadda ya cece mu, da yadda yana so mu yi rayuwarmu. Yana ƙunshi da alkawarai da yawa na kasancewarsa da albarku tare da gargaɗai da umarnai domin rayuwar kowace rana.

A cikin wannan darasi, za mu ga wata sashe ta Zabura 119 sura ce mafitsawo a cikin Littafi Mai Tsarki, domin ganin muhimmancin nawaya Kalmar Allah a cikin rayuwar mai bi. Wannan Zabura tana ɗauke da kan magana 22 na ayyoyi 8 na kowace saƙo na baƙaƙke 22 na harufan Ibraniyawa. Kan maganar Zabura 119 shi ne 'Kalmar Ubangiji' da waɗansu makammantan da aka yi amfani da su akai –akai domin kwatanta kalmar Allah: doka, da ƙa'idodi, da umarnai, da farillai, da dokoki, da kalma da alkawarai.

A ƙarshen wannan darasi, za ka nuna maka **karin bayani** A, B, da C inda za ka koya waɗansu jogarar da aka saba yi domin a kafa tsarin ayyukan binciken Littafi Mai Tsarki, hanya mai sauƙi na bi da kanka kowace ranar bincike da waɗansu tambayoyin sa cikin aiki domin yǎ taimake ka amfani da abin da ka koya.

### Karanta Zabura 119:1-40 a hankali.

① **Sāke karanta ayyoyi 1-8.**

Menene waɗannan ayyoyi suke koyar game da biyayya da kalmar Allah?

② **Sāke karanta ayyoyi 9-16.**

Yaya mai girma cikin bi zai yi rayuwar tsarkin da zai girmama Allah?

Hanyoyi da yawa domin girma cikin ƙauna da ganewar kalmar Allah an kwatanta a cikin wannan shafi. Nemi ayyoyin da suka kwatanta waɗannan ayyuka a cikin ayyoyi 9-16 ka kuma rubuta gajeren kwatanci na kowanensu.

Bincike: Ayyoyi:__________________________

Kwatanci:

Haddacewa: Ayyoyi:__________________________

Kwatanci:

Nazari: Ayyoyi:__________________________

Kwatanci:

Muddin muna da ganewar abin da Allah yake bukata daga gare mu, yana da muhimmanci cewa mu yi biyayya. Sa zuciya a kan ƙaunar Allah da yin rayuwa cikin biyayya ga ƙa'idodin da aka samu a cikin Kalmar Allah yana taimaki masu bi rayuwar tsarki.

③ **Sāke karanta ayyoyi 17-24.**

Menene sashen Allah da kuma ina sashenmu a cikin ganewar Kalmarsa?

Sāke tuna da abin da mun koya game da Allah Ruhu Mai Tsarki a cikin darasin da ya wuce. Yaya ya taimaka musamman wa mai bi, yă gane da Kalmarsa? (dubi Yohanna 14:25-26; 16:12-14)

Yi addu'a yanzu cewa Allah, ta wurin Ruhu Mai Tsarki, zai taimake ka ka gane wannan darasi.

④ **Sāke karanta ayyoyi 25-32.**

Yaya ne Kalmar Allah tana taimke mu a lokacin damuwa? (25-32)

⑤ **Sāke karanta ayyoyi 33-40.**

Yaya Kalmar Allah take canja mu?

Yaya mai bi zai ba Kalmar Allah muhimmancin da take bukata a cikin rayuwarsa ta yau da kullum?

## Ayyukan ra'ayi

1. Duba abubuwan da suke cikin Littafi Mai Tsarki tare ku auna bambancin sassan da yake ɗauke da shi. Sa'an nan, ku kalla finafinen Summary of the Bible (Littafi Mai Tsarki a taƙaice).
2. Kalla finafinen How to read the Bible (yadda za a karanta Littafi Mai Tsarki) mai bayana yadda Littafi Mai Tsarki. Tattauna a zaman ƙungiya yadda za ka iya sa cikin aiki ko inganta karatun kowace rana na Littafi Mai Tsarki.
3. Kalla finafinen The Bible explored (Binciken Littafi Mai Tsarki) bayana yadda Littafi Mai Tsarki ya zo mana cikinkarnai.
4. Kalla finafine Is the Bible trustworthy? (Ko Littafi Mai Tsarki ya cancanta?) Tattauna wannan a zaman ƙungiya. Sa'an nan, ɗauki waɗansu lokaci domin godiyar Allah saboda kiyayewar Kalmarsa cikin dukan karnai domin tabbatarwar da za mu iya samuwa bai taɓa gurɓata ba.

## Sa cikin aiki: Yaya za mu zurfafa dangantakarmu da Allah ta wurin Kalmar Allah?

1. Yesu ya faɗa a cikin Matiyu 4:4: "Ba da abinci kaɗai mutum zai rayu ba, sai dai da kowace kalmar da take fitowa daga wurin Allah." Bisa wannan ayya, yaya za ka gama wannan jumla:

   "A zaman cin abinci kowace rana yana da muhimmanci ga jiki domin yǎ ci gaba da girma,

   ___

   ___

   Ko yana da muhimmanci kowace rana mutum yǎ sami halin ɗauki lokaci cikin Kalmar Allah da addu'a. Babu ƙa'idodin da aka kafa domin samun lokaci da Allah. Amma akwai waɗansu jagora masu kyau da ayyukan da za ka sa ciki aiki domin inganta wannan hali.

   – Dubi **Karin Bayyani A** domin waɗansu buɗe ido a kan kafawar binciken kowane lokaci.
   – Dubi **Karin Bayani B** domin misalin hanyar binciken Littafi Mai Tsarki domin amfanin Zabura 119:105.

- Dubi **Karin Bayani C** domin jerin tambayoyi ka tambayi kanka domin yă taimaka sa abin da ka koya cikin aiki.
- Dubi **Karin Bayani G** saboda ra'ayin karatun Littafi Mai Tsarki kowace rana domin inganta ganewar Kalmar Allah.

2. Wannan mako, idan ba ka riga ka yi ba, ka kafa binciken Littafi Mai Tsarki na yau da kullum. Kowace rana, ka rubuta abin da ka koya da wane tasiri wannan yana da shi a kan rayuwarka. Shirya za ka faɗa wannan wa sauran ƙungiya mako mai zuwa.

## Faɗa

Wannan mako, faɗa wa waɗansu abin da ka koya a cikin wannan darasi. Za ka iya maimaita darasin da wani.

# Darasi ❸: Addu'a - Magana da Uba

## Matiyu 6:5-15

Suna: ________________________________________ Kwanan wata: ______________________

## *Manufofin Daarasi*

1. *Gane zarafi da muna da shi a zaman 'ya'yan Allah mu zo wurin Ubanmu a cikin addu'a.*
2. *Dubi addu'ar Ubangiji a zaman tushen gurbi domin addu'a ta kowace rana.*
3. *Ɗanɗana canjin zuciyarmu ta dalilin addu'a (Filibbiyawa 4:6-7).*

✧

### Yaya Kake Ci gaba a kan?

1. Menene muhimman kalmomin darasi na ƙarshe?
2. Menene ya faru lokacin da ka faɗa wa ɗansu abin da ka koya?
3. Menene ya canja a cikin rayuwarka ta dalilin waɗannan koyarwa?

### Karanta Matiyu 6:1-15 a hankali.

**MA'ANA**:

- Girmamawa: domin girmama a zaman tsarki
- Jarabawa: jan hankali (zugi) domin aikata mugunta ko a lokacin gwaji.

Wane hali ne ya kamata almajirin Yesu ya riƙe lokacin addu'a? (5 da 6)

---

Ta wurin wane suna ne ya kamata masu bi su yi magana da Alla cikin addu'a (ayya 9)?

---

A cikin ayya ta biyar, Yesu ya yi magana da ƙungiyar mutane: sa'ad da ku yana nuna (da yawa) yi addu'a… Amma a cikin ayya 6, ya mai da addu'ar tasa: ka (ɗaya) yi addu'a…' yana nanata cewa addu'armu ya kamata yă kasance cikin siri, tsakannimu da Allah.

Mene ne ya ba mu wannan zarafi? (Dubi Yohanna 1:12)

---

Menene Yesu ya koyar game da maimaitawar Magana mara anfani?

---

Saboda wadanne roƙo uku ne aka gargaɗe mu domin addu’a a cikin ayoyyi 9 da 10?

1.

2.

3.

---

Idan na yi addu’a da gaskiya domin waɗannan abubuwa, yaya rayuwana zai yi tasiri?

---

Yaya Yesu ya koya mana mu yi addu’a saboda bukatunmu (11)?

## Karanta kuma Filibbiyawa 4:6-7.

Mene ne Ubanmu na sama ya yi alkawari gare mu sa’ad da muka miƙa bukatunmu gare shi?

---

Yesu ya koya mana cewa ya kamata mu roƙe Ubanmu na cikin sama yă gafarta mana kullum. Don me yana da muhimmanci?

---

Mene ne ya kamata yă zama halayanmu na zuciya zuwa waɗanda suka yi mana laifi?

---

Mene ne sakamakon ruhun rashen gafartawa? (Matiyu 6:12-15)

---

Don me yana da muhimmanci a taru domin mu yi addu'a da waɗansu? (Matiyu 18:18-20)

---

Menene ka koya a cikin wannan darasi wanda zai taimake ka a cikin rayuwar addu'arka?

## Ayyukan ra'ayi

1. Yaya ne gargaɗin da Yesu ya bayar game da addu'a yana dabam da abin da ake yi kewaye da kai? Don me kake tunani cewa babu abin da aka ambata game da al'adar wanka, matsayin da za a nema, inda za a fuska, lokuta cikin yini ko yaren da za a yi amfani domin addu'a? Tattauna wannan a zaman ƙungiya.
2. Idan ba ka san addu'ar Ubangiji da kai ba, koya yanzu (yi amfani da juyin da ake amfani da shi a cikin Ikkilisiyarka).
3. Kalla wannan rubutu game da addua'r Ubangiji. Tattauna abin da ka koya game da shi. Sa'an nan yi addu'ar Ubangiji tare ku tsaya bayan kowane jumla a zaman nazari a kan ma'anar jumlar.
4. Yi addu'a ka roƙi Allah yo nuna maka abin da damuwa akai. Ku rarrabu cikin ƙungiyoyi biyu ko uku ku faɗa (musamman ko abin da ya shafi kowa da kowa yadda kuke so) game da waɗanan yanayi. Yi addu'a domin juna. Ku kamala da rerawa daga waƙoƙi Turn your eyes upon Jesus ('Kafa idanunka a kan Yesu') ko reran a zaɓinka a kan wannan kan magana.

## Aikatawa (Sa cikin aiki): Yaya za mu zurfafa dangantakarmu da Allah ta wurin Kalmar Allah?

1. Ɗauka ɗan lokaci domin addu'a tare na addu'ar Ubangiji ta wurin yin amfani da gurbin da yake ƙasa:
   - **Sujada (ayya9):** Zo wurin Allag a zaman Uba, gode masa cewa kai ɗansa. (minti 5)
   - **Miƙa kai (ayya 10):** Miƙa kanka ga nufinsa da addu'a cewa za ka yi nufinsa a cikin sassa dabam-dabam na rayuwarka. (minti 5)

- **Roƙe-roƙe (ayya 11):** Kawo bukatunka a gare shi tare da imani cewa zai tanada. Yi addu'a kuma domin bukatun waɗanda suna kewaye da kai. (minti 10)
- **Furci (ayya12):** Furta duk zunubinka wanda kana sane ka kuma roƙe shi gafararsa. Haka kuma, ka tabbatar ka gafarta wa duk wanda ya yi maka laifi. (minti 5)
- **Tsare (ayya 13):** Roƙi Allah yă riƙe ka da hannunsa na tsare kewaye da kai kuma yă ƙarfafa ka domin tafiya a cikin nufinsa. (minti 5)
- **Godiya:** Rufe da ba da lokacin godiya da ƙara tabbatarwar ƙaunarka gare shi. (minti 2)

2. Wannan mako, ka keɓe lokaci na musamman kowace rana domin addu'a. Ka yi amfani da jagora/gurbin da aka bayar a cikin wannan darasi. A cikin **Karin Bayani D,** akwai kuma jerin ayyukan addu'o'i dabam –dabam wanda za ka fara amfani da shi domin inganta addu'arka. Bisa ƙari kuma, dubi **Karin Bayani G,** domin ra'ayin da aka bayar karanta Littafi Mai Tsarki kowace rana domin ƙara zurfin ganewar addu'arka. Rubuta abin da ka koya da yadda addu'a ya taɓa rayuwarka. Shirya domin ka faɗa wannan ga sauran a cikin ƙungiyarku mako mai zuwa.

## Faɗa

Wannan mako, faɗa wa waɗansu abin da ka koya a cikin wannan darasi. Za ka iya maimaita darasin da wani.

# Darasi ❹: Azumi da Nazari - Matsowa Kurkusa da Uban

**Matiyu 6:16-18**

Suna: ________________________________________ Kwanan wata: ______________________

## *Manufofin Darasi*

1. *Arzuta zaman kurkusanmu da Allah ta wurin bincike da aikata horarwar ruhaniya ta hanyoyi dabam-dabam.*
2. *Gane azumin koyarwar Littafi Mai Tsarki da dangantakarta domin addu'a.*
3. *Kara marmari mu ba da lokaci mu jira Allah a cikin addu'a.*

✧

### Yaya Kake Ci gaba a kan?

1. Menene muhimman kalmomin darasi na ƙarshe?
2. Menene ya faru lokacin da ka faɗa wa ɗansu abin da ka koya?
3. Menene ya canja a cikin rayuwarka ta dalilin waɗannan koyarwa?

Marubucin Zabura ya rubuta: "Kamar barewa take marmarin ruwan rafi, haka raina yake marmarinka, ya Allah." (Zab 42:1)

A cikin wannan darasi, za mu tarar da aikata waɗansu koyarwar Littafi Mai Tsarki wanda sun taimaka mana mu yi addu'a da zurfi cikin zumuntarmu da Allah, Ubanmu na cikin sama.

## AZUMI

A cikin Littafi Mai Tsarki, azumi koyaushe yana tafe da addu'a musamman lokacin bukata da rikici:

- Musa ya yi azumi kwana 40 ba tare da ci ko sha ba (Fit 34:28) kafin yǎ karɓa dokoki 10.
- Dawuda ya yi kwanaki bakwai (2Sam 12:16,21) yana roƙo ga Allah ya tsare ran ɗansa daga ciwo.
- Esta ta roƙa domin a yi azumi na kwana uku kafin ta kai roƙo a gaban sarki domin mutanenta (Esta 4:16).
- Kristi bai ci kome ba cikin kwanaki 40 na jarabawa ta wurin Shaiɗan. (Luka 4:2).

### ① Anna, Annabiya

### Karanta Luka 2:36-38.

Yaya Anna ta yi sujada ga Ubangiji?

Menene ka yi tunanin da ya motsa ta domin ta miƙa kanta cikin addu'a da azumi?

---

Wane ladan babu shiri ne ta karɓa? (Ayya 38)

---

## ② Ikkilisiyar Antiyok

### Karanta Ayyukan Manzanni 13:1-3.

Menene ya faru a lokacin da shugabanen ikklisiya a Antyok suna bowtawa Ubangiji da Azumi?

---

Wannan lokacin juyawar Ikkilisiya a cikin tarihi. Krista masu bi sun fara shaidar bangaskiyarsu a zaman hali da iyalinsu da abokansu. Amma wannan shi ne farawar fita cikin yarda zuwa sababbin garuruwa da ƙasashe. Ta wurin Ruhu Mai Tsarki, Allah ya sha gana a lokacin addu'a da azumi domin a fara sabon aiki.

Don me ka na tunani sun ƙara yin azumi da addu'a kafin su aika Barnaba da Shawulu a kan hanyarsu?

---

## ③ Yesu ya yi koyarwa game da azumi

### Karanta Matiyu 6:16-18.

Yesu ya sa rai almajiransa za su yi azumi da addu'a?

---

Menene manufar azumin nan?

---

Yaya Yesu yana so mu nuna hali lokacin azumi? Cika waɗannan wurare wadda sun kwatanta daidai da halin bai dace ba a lokacin azumi.

| | Azumin riya | Azumin bisa ga Yesu |
|---|---|---|
| **Ganin fuska** | Ɗara fuska da bushewar baki | |
| **Manufa** | | Domin neman fuskar Allah |
| **Lada** | | |

Yanzu a cikin kalmominka, kwatanta irin azunin da shi ne gaskiya na faranta wa Allah rai.

Ta wurin ajiiye ƙwarewa a gefe na rayuwar yau da kullum na ayyukan da ya kamata a yi su da jin daɗi, azumi yakan ba mu karin lokacin da Allah cikin addu'a. Zai iya ƙara marmarin neman saduwa da Allah. Azumi kuma yana ba mu babban zarafi domin nazari a kan kalmar Allah.

## JIRA UBANGIJI DA YIN NAZARI A KAN KALMARSA

Sa'ad da muna jiran Ubangiji, za mu ba da hankalinmu a kansa domin shi ne zai iya bayyana kansa gare mu. Muna ɗauki lokaci a wurin addu'a domin mu ƙuƙƙulle damuwowin wannan duniya. Manufarmu domin mu iya karɓa kowane saƙon Ubangiji wanda zai zuga tunaninmu ko mu gane kasancewarsa. Irin saƙon nan ya kamata koyaushe ya kasance bisa koyarwar kalmar Allah.

Saboda haka, lokacin jiran Ubangiji, zai kasance da taimako a gare mu mu yi nazari a kan kalmarsa. Karanta ayya ko shafofin Littafi Mai Tsarki sa'an nan a ɗauki lokaci ana tunani game da ma'anar. Menene ya koyar game da Allah da dangantakarsa da kai? Wannan zai iya yi maka jagora cikin lokacin yabo.

## ④ Yunwa domin Allah

**Karanta Zabura 63.**

Yaya mai Zabura ya kwatanta marmarinsa domin kasancewar Allah?

Kwatanta hanyoyin da mai zabura ya nemi Allah.

---

Mai Zabura ya yi marmarin yin kurkusa ga Allah yayin da yana ɗanɗana kasancewarsa a cikin haikali (wurin kasancewar Ubangiji). Yau muna iya ɗanɗana yin kurkusa ko'ina yayin da muka yi tunani a zuci da kuma sujada ga Yesu.

Wane riba ne mai Zabura ya karɓa daga neman Allah?

## Ayyukan ra'ayi

1. Faɗa abinda ka dandana cikin azumi da addu'a ga waɗansu a cikin ƙungiya.
2. Yaya koyarwar azumi na Littafi Mai Tsarki ya yi kamma/dabam da azumin da waɗansu suke aikatawa a cikin ganewarsu? Tattauna wannan a zaman ƙungiya.
3. Tattauna don me kana tunani Krista da yawa ba sa sāke yin azumi kuma.
4. Horarwar azumi zai iya zama da kyau sosai dominmu a jiki haka ma a ruhaniya. A samu wani a cikin ƙungiyarku ya bincika ribar da ake samu a jiki ya faɗa a cikin ƙungiya.

## Aikatawa (Sa cikin aiki): Yaya za mu zurfafa dangantakarmu da Allah ta yi zurfi ta wurin azumi da Nazari?

1. Ɗauka lokacin azumi da addu'a da niyya sosai. Ko ƙasarka, Ikkilisiyarka, ko iyali za su bukaci jagora ko akwai bukatu ta musamman? Kafin ka miƙa kai cikin yin azumi, tuntuɓi **Karin Bayani E** a ƙarshen wannan kos domin jagorar azumi da sharhi na zaman lafiya.
2. Yi nazari kowace rana a makon nan a kan shafin Nassi a cikin bincikenka da lokacin addu'arka. **Karin Bayyani G** a ƙarshen yadda wannan kos ya tanada maka a cikin ayya domin kowace rana na makon nan cewa wanda an riga an zaɓa domin yǎ zurfafa ganewar azumi da nazari.

## Faɗa

Wannan mako, faɗa wa waɗansu abin da ka koya a cikin wannan darasi. Za ka iya maimaita darasin da wani.

# Darasi ❺: Ikkilisiya-Sabuwar Iyalinmu

## Ayyukan Manzanni 2:42-47

Suna: ________________________________________ Kwanan wata: ______________________

## *Manufofin Darasi*

1. *A gane cewa mu sashi na iyalin masu bi ne a duniya duka.*
2. *A koya daga Ikkilisiyar Yerushalima muhimmin ayyukan zumuntar Ikkilisiya.*
3. *A gane yadda ake sa cikin aiki ƙa'idodin koyarwar Littafi Mai Tsarki a kan bayarwa.*
4. *A miƙa kai cikin Ikkilisiya jikin Kristi.*

✧

### Yaya Kake Ci gaba a kan?

1. Menene muhimman kalmomin darasi na ƙarshe?
2. Menene ya faru lokacin da ka faɗa wa ɗansu abin da ka koya?
3. Menene ya canja a cikin rayuwarka ta dalilin waɗannan koyarwa?

A cikin darasssuna hudu na farko, mun dubi wurin da Ruhu Mai Tsarki, da Kalmar Allah, da addu'a, da azumi da nazari a cikin rayuwar sabon mai tuba. Amma ba mu kaɗai a cikin ƙoƙawar nan domin rayuwa saboda Kristi mai Cetonmu a cikin duniyar nan mai tashin hankali ba. An haife mu a cikin sabon iyali da 'yan'uwa maza da mata.

A cikin wannan darasi, za mu ga yadda wannan ya kawo mana babban zarafofi amma da muhimmancin nawaya. A zaman memba na sabon iyalin, me za ka yi da kuma yaya za mu amfana?

### ① Bautar Allah tare: Ikkilisiya Ta Farko

### Karanta a hankali Ayyukan Manzanni 2:42-47.

Waazin manzo Bitrus mai iko a ranar Fentekos ya kai mutane 3000 sun karɓi Ubangiji Yesu da kuma yin baftisma. Menene muhimman ayyuka huɗu wadda masu bi sun miƙa kansu? (ayya 42)

1.

2.

3.

4.

---

**Koyarwar Manzanni:** Waɗannan masu bi ba su da Littafi Mai Tsarki kamar yadda muke da shi yau. Manzanni suka koyar da su cewa Yesu shi ne Kristi wanda ya cika annabcin Tsohuwar Yarjejeniya. Sun iza su domin su tuba a kuma yi musu baftisma a cikin sunan Yesu domin gafarar

zunubanmu. Sun koya musu game da koyarwa da rayuwar Yesu. Yau koyarwarsu shi ne yana samuwa a cikin Sabuwar Yarjejeniya.

**Kaƙƙaryawar gurasa:** Wannan shi ne sashen sujada na Krista na farko. Masu bi sun tuna da jibin Yesu na ƙarshe da almajiransa. Sun yi godiya domin mutuwarsa da tashinsa daga matattu da kuma biki kasancewarsa tare da su. (Luka 24:30-35; Ayyukan Manzanni 20:7)

Kowane daya daga cikin waɗannan muhimman ayyuka duka zarafi ne da kuma nawaya. Cika wannan wurare a ƙasa, a cika kowane shafi

| Ayyuka | Zarafi | Nawaya |
|---|---|---|
| Koyarwar Manzanni | Domin a koya babbar gaskiyar bangaskiyar Krista | Domin a saurara a hankali a kuma sa koyarwa a cikin aiki. |
| | Domin a karɓi taimako da ƙarfafawa daga sauran. | |
| Kakkarya gurasa | | Domin mutum yă shirya kansa domin sujada da gaskiya.<br>Domin yin aiki mutane su tattaru domin sujada |
| | | |

Mun karanta yadda masu bi sun sayar da mallakarsu da kuma kaya domin su taimaka wa yanúwansu masu bi. Wannan shine hanyar gaskiya na zumuntarsu. Ko za ka iya tuna da wadansu hanyoyi wadda baye-bayen kudinsu ya wajiba da kuma muhimmanci?

Yaya masu bi suka yi amfani da gidajensu?

Menene ya zama tsarin masu bi a kan alúmma? (aya 47)

---

## ② Bayarwa ga Allah ta wurin Ikkilisiyar Iyalinmu

Mika kai da kuma baye-baye na Ikkilisiyar farko na Urushalima yana kayatarwa. Duk da haka bai zama abin koyi ne ga dukan masu bi su sayar da dukan mallakarsu ba. A cikin 2 Korintiyawa sura 8 da 9, Bulusbya bayyar da muhimman jagora akan yadda zaa bayar.

**Karanta 2 Korintiyawa 9:6-12.**

Yaya bangaskiyarmu ya shafi bayarwa ga iyalinsa?

---

Yanzu a ba da hankali a kan ayya 7 yayin da kake ba da amsar waɗannan tambayoyi:

- Wanene zai bayar?
  - ☐ Waɗanda suke da arziki sosai.
  - ☐ Waɗanda suke da bukata domin kafarar zunubansu.
  - ☐ Dukan masu bi.
  - ☐ Waɗanda suke so.
- Nawa ne za mu bayar? (dubi 1 Kor 16:1-2)

---

- Wanene zai ba da ra’ayi

---

- Menene ya kamata yă zama halinmu?

---

Dole da farin cikine za mu ba da baiko da farkon farawa cikin sujada ga Allah, sa'an nan zuwa zumuntar Ikkilisiya domin rabawa bisa bukatu.

## ③ Karfafa juna ta wurin Ikkilisiya

### Karanta Ibraniyawa 10:23-25.

Marubucin wasiƙar Ibraniyawa ya damu cewa waɗansu abokansa sun tsaya da saduwar da aka saba yi domin sujada tare. Sun jimre wahala da tsananni. Waɗansu sun rasa kayakinsu har an wulaƙantar da su (10:32-34). Wataƙila su fuskanci kisan gilla domin bangaskiyarsu (12:4). Ya ƙarfafa su kada su karaya.

Don me yana da muhimmanci cewa mu ci gaba da saduwa tare?

### Ayyukan ra'ayi

1. Kalla finafine What constitutes a real church? (Abin da ya ƙunshi Ikkilisiyar gaskiya?) Yaya mutane a cikin al'ummarka suna ganin Ikkilisiya? Menene ya canja a cikin hanyar da kake gani ta wurin darasin yau? Tattauna wannan a zaman ƙungiya.
2. Saurari addu'a cewa Yesu ya yi addu'a domin almajiransa kafin a kama shi. Yayin da ka saurara, rubuta abin da Yesu ya roƙi Uban domin almajiransa. Menene yake da muhimmanci a gare shi? Sa'an nan, yi addu'a domin iyalin almajiranka.

### Aikatawa (Sa cikin aiki): Yaya za mu zurffafa dangantakarmu da Allah ta yi zurfi ta wurin miƙa kai cikin Ikkilisiya?

1. Sāke duba zānen ayyukan Ikkilisiyar Yerusalem, da nawayoyinta da zarfofinta. Lura da kowane ayyuka a hankali. Sa'an nan a tattauna waɗannan tambayoyi:
   a) A cikin wane hanyoyi ne za ka fi samun amfani fiye da zarafofin kowane ayyuka?
   b) A cikin wane hanyoyi ne za ka ƙara ɗaukar nawaya?
2. Wannan mako, ka inganta shirin bayarwarka bisa ƙa'idodin wannan darasi. Duba **Karin Bayyani F** a ƙarshen wannan kos domin hanyoyin jagora domin taimake ka shirin bayarwarka.
3. Kowace rana na makon nan, yi amfani da ra'ayi karatun Littafi Mai Tsarki a cikin **Karin Bayyani G** domin ƙara zurfin ganewar ƙa'idodi a cikin wannan darasi wanda ya ƙunshi Ikkilisiya.

## Maimaicin na Kos 102

Maimata darusan wannan Kos. Sa'an nan, ka faɗa shaidarka na abin da suka koya lokacin wannan Kos, da yadda ya shafi raywarsu.

## Faɗa

Wannan mako, faɗa wa waɗansu abin da ka koya a cikin wannan darasi. Za ka iya maimaita darasin da wani.

# Karin Bayanai

## *Darasi 2: Kalmar Allah*

### Karin Bayani A: Hanyoyin Jagora da Aikatawa domin Tasirin Binciken Littafi Mai Tsarki

- A sa lokaci da wurin saduwa da Allah shi ne mataki na farko a cikin inganta wannan hali.
- Wani aiki mai kyau shi ne a fara da lokacin addu'a, roƙi Ruhu Mai Tsarki yǎ buɗe zuciyarku domin ganewa da yi amfani da kalmarsa.
- Yayin da ka karanta Kalmar Allah kowace rana, tuna da hanyoyi uku wanda muka samu a cikin Zabura 119:9-16, wanda za ka iya rayu a kan Kalmar Allah.

  1) **Bincike:** a hankali ka duba, ka auna ka kuma nema domin ka gane Kalmar Allah
  2) **Hadaccewa:** maimaita kalmomin Nassi har sai ka koya da kai (tuna da kowace kalma)
  3) **Nazari:** maimaita ko hadaccewar Nassi da kuma tunani a kan ma'anar shafi da kuma aikin ta a cikin rayuwa. Wannan shi ne ƙarfafawa cikin dukan yini da kuma buɗe hanyar ta wurin hadaccewar Nassi.

## *Darasi 2: Kalmar Allah*

### Karin Bayani B: Tasirin Hanyar Binciken Littafi Mai Tsarki

- **Ga hanyar binciken Littafi Mai Tsarki mai sauƙi da za ka yi amfani da shi kowace rana domin taimako ka gane ka kuma yi amfani da Kalmar Allah.**

1) **Sujada:** Fara da yabon Allah da kuma roƙe shi yǎ bayyana kansa gare ka. (minti 3)

2) **Binciken Littafi Mai Tsarki:** Neman ganewar shafin da ka zaɓa.
   a. Duba shafi (minti 5)
   b. Bayana ma'anar shafi (minti 5)
   c. Amfani da koyarwar a rayuwarka (minti 5)

3) **Rufe da addu'a**, fara da gyara a shafin Littafi Mai Tsarki da abin da ka koya a cikin bincike. (minti 5)

- **Kasa shi ne misalin wannan binciken Littafi Mai Tsarki ta wurin amfani da Zabura 119:105:**

1) **Sujada:** Fara ta wurin yabon Allah da roƙonsa yǎ bayyana kansa a gare ka. (minti3)

2) **Binciken Littafi Mai Tsarki:** Neman ganewa Zabura 119:105.
   a. Duba Shafin (minti 5)
      - Ins muhimman kalmomi da mai Zabura ya yi amfani ya kwatanta tasiri/muhimmanci Littafi Mai Tsarki a cikin rayuwarsa?
      - Karanta sauran ayyoyi a cikin wannan yanki Zabura (ayyoyi 105-112). Yaya za su taimake mu, ganewa da kyau abin da mai Zabura ya faɗa a cikin ayya 105?
      - Yanzu ka rubuta tambayar kanka abinda ka duba ka kuma ba da amsa.
   b. Bayana ma'anar rubutun. (minti 5)
      - Yi tunani game da muhumman kalma ɗaya ko biyu na mai Zabura wanda ya yi amfani da su ka kuma rubuta don me ya zaɓe su su kwatanta tasirin Kalmar Allah a kan rayuwarsa.
      - Yaya mai Zabura ya zama misali a gare mu a cikin miƙa kansa yǎ bi koyarwar Littafi Mai Tsarki? (ayya 105-112)
      - Yanzu ka rubuta tambayar tafintarka kuma ka ba da amsa.
   c. Kayi amfani da koyarwar a rayuwarka (minti 5)
      - Ka ƙara karanta ayyoyi 107 da 110. Kana ɗanɗana gāba kamar yadda Dawuda ya samu lokacin da ya rubuta su?
      - Hadacce Zabura 119:105. Maimaita ta da farko kowane safe na wannan mako da kuma ƙarshe abu kafin tafiya barci da dare, sa'an nan tsakannin kowane ayyukan yini. Gode wa Ubangiji domin Kalmarsa ka kuma roƙe shi yǎ amfani da ita domin jagorar ka.
      - Zaɓi wani abin da mai Zabura ya yi (105-112) tare da Littafi Mai Tsarki ka yi kwaikwayonsa a cikin rayuwarka.

3) **Rufe da addu'a**, fara da gyara a cikin wannan ayya da abin da ka koya daga bincikes (minti 5)

## *Darasi 2: Kalmar Allah*

### Karin Bayani C: Tambayoyin amfani da binciken Littafi mai Tsarki

- Kasa shi ne jerin tambayoyi masu kyau wanda za ka iya yi sadda kana ƙoƙari domin ka gane yadda za ka yi amfani da Littafi Mai Tsarki a cikin rayuwarka kullum:

1) Akwai **misali** domina in bi ko kada in bi?

2) Akwai **zunubi** domina in bari?

3) Akwai **alkawari** domina in riƙe?

4) Akwai **addu'a** domina in yi?

5) Akwai **umarni** domina in yi biyayya?

6) Akwai **sharaɗi** domina in biya bukatar?

7) Akwai **ayya** domina in hadacce?

8) Akwai **kuskure** (koyarwa/tauhidi) domina in bari?

9) Akwai **kalubala** domina in fuskanta?

10) Akwai wani abin da zai **taimakeni in dage** da yanayin da nake ratsewa a ciki?

11) Akwai wani abin da nake bukata domin in **faɗa** wa waɗansu….
    a. A cikin iyalina
    b. A cikin zumuntar Ikkilisiyata
    c. A cikin dangantakana ko saduwa da marasa bi?

## *Darasi 3: Addu'a*

### Karin Bayani D: Ayyukan Addu'a

- Kasa shi ne jerin ayyukan addu'a wanda za ka yi amfani da shi a cikin rayuwarka kullum lokacin addu'a ga Allah (daidaitawa daga Dick Easrman "Awar da ta na Canza Duniya")
  - **Yabo da sujada –** furta ƙaunarka ga Allah domin yadda an san shi da kuma abin da ya yi.
  - **Jiran Ubangiji –** lokacin nazari akawaice inda za ka yi shiru da kewayenka ka kuma jira a cikin kasancewarsa.
  - **Furtawa –** cikin ƙasƙanci kana auna kanka da karɓa zaman mai zunubi a gaban Allah da karɓi tsabtaccewar zunubinka bisa mutuwar Yesu a kan gicciye.
  - **Nassin Addu'a –** yi addu'a ta wurin amfani da shafin Nassi yana taimaka ciyar da kanka daga kalmar Allah. Za ka yi addu'a cewa Allah zai cika nufinsa a cikin rayuwarka/ki ko a cikin waɗanda ka/kin ambata da suna.
  - **Tsaro –** lokacin dubawa ta ruhaniya yayinda kana/kina tambayar Allah yă nuna maka shirinsa ko abin yi musamman a yanayin da kake/kike zaman tsaro domin girmamawar Ubangiji.
  - **Adduár godo –** tsayawa a tsakanni a madaddin wani da addu'a domin bukatun mutumin nan ko yă kasance ceto, ko jiki, ko ruhaniya, ko bukatar tunani.
  - **Roƙo –** kawo roƙon bukatunka/ki ga Allah
  - **Godiya –** kawo godiyarka/ki domin kulawar Allah, ta wurin tsaro, da albarka, da yin kirki gareka/ki.
  - **Waƙoƙi –** furta ƙaunarka, da sujada ko ɗaukaka ga Allah cikin rerawa.
  - **Nazari –** lokaci maimaita ko binbini a kan Nassi da tunani a kan ma'anar shafi da kuma amfaninsa ga rayuwa.
  - **Saurara –** lokacin yin shiru na zaman kame kai a gaba Allah kana neman gargaɗi ko hanyar da za ka bi daga wurin Ubangiji.

Yanzu kana iya shirya lokacin addu'arka ta wurin amfani da jerin ayyukan addu'a da ke bisa. Ana misali: Kana iya yin addu'a na awa ɗaya, ka ɗauki lokacin addu'a minti 5 a kan kowace ayyukan addu'a.

- Bisa ƙari, kana iya amfani da lokacin addu'a ka bi jerin tsari a bisa a kan addu'ar da Yesu ya koya wa almajiransa a cikin Matiyu 6 wadda mun yi amfani da shi a ƙarshen darasi 3. Ɗauki ɗan lokaci domin addu'a cikin addu'ar Ubangiji yi amfani da tsarin da yake ƙasa:
    - **Sujada (ayya 9):** Zo wurin Allah wanda shine Uba, gode masa a kan cewa kai ɗansa ne. (minti 5)

    - **Miƙa kai (ayya 10):** Miƙa kanka ga nufinsa da addu'a cewa nufinsa zai cika a sassan rayuwarka dabam-dabam. (minti 5)

    - **Roƙo (ayya 11):** Kawo bukatunka/ki gare shi tare da imani cewa zai tanada. Yi addu'a kuma domin bukatun waɗansu kewaye da kai. (minti 10)

    - **Furtawa (ayya 12):** Furta duk zunubin da ka sani kuma ka roƙe shi gafara. A lokaci ɗaya, ka tabbatar ka gafarta wa duk wanda ya yi maka laifi. (minti 5)

    - **Kariya:** Tambayi Allah ya kewayeka/ki da hanunsa na kariya kuma ya karfafa ka/ki domin tafiya cikin nufinsa.

    - **Godiya:** Ka rufe da lokacin nuna godiya da ƙara tabbattar da ƙaunarka/ki gare shi. (minti 2)

## *Darasi 4: Azumi da Nazari*

### Karin Bayani E: Jagorar Yin Azumi

- Kasa waɗansu tambayoyi ne waɗanda kana iya yi wa kanka domin taimako ka fara shirin azumi da waɗansu jagora domin su taimake ka ka yi azumi lafiya.

1. **Menene manufar azuminka/ki?**
   a) Domin neman Allah cikin sujada
   b) Domin neman taimako a lokacin damuwa
   c) Domin neman albarkar Allah da kariya a kan aikin Krista
   d) Waɗansu dalilai na kaina

2. **Wane irin azumi zai cancanta da kai.**
   a) **Azumin da aka saba**: babu abinci, amma kana iya shan ruwa.
   b) **Azumin haka kawai**: hana kanka daga waɗansu irin abinci (ana misali: Daniyel ya hana kansa daga cin abinci sarki – Daniyel 1:8-16). Wannan yana da kyau domin waɗanda suke da damuwar lafiya (misali: ciwon siga) wanda azumin da aka saba zai zama da damuwa.
   c) **Cikakken azumi**: Babu abinci ko ruwa (Misali: Musa a kan Tundun Sinai – Fitowa 34:28; M. Sha 9:9,18). Kana iya yin lura sosai da irin wannan irin azumi. Ya kamata ka tsayar da azumin ka nemi taimakon likita idan waɗansu alamu na musamman sun fito. Wannan irin azumi ya kamata yă kasance na gajeren lokaci.

3. **Na tsawon lokaci nawa ne za ka yi azumi?**
   a) Na irin abinci ɗaya
   b) Na safe zuwa yamma
   c) Na cikakken awa 24 (tsakar dare zuwa tsakar dare).
   d) Na kwanaki. Ka yi hankali da wannan lokacin azumi ka kuma tsayar da azumi ka nema taimakon likita idan alamu na musamman sun fito.

4. **Wane irin ayyuka ne za ka ba da hankali a kai lokacin azumi?**
   a) Addu'a-yi addu'a tare jerin abubuwan da kake/kike so ka/ki kawo a gaban Allah
   b) Yi nazari a kan Kalmar Allah-ɗauki shafi domin bincike
   c) Jiran Ubangiji- ka sami inda kana iya tafiya wurin da babu surutu.

## *Darasi 5: Ikkilisiya*

### Karin Bayani F: A Shirya Hanyar Bayarwa

(daidaita daga 'Grandir en tant ƙue Disciple' Formation du Disciple, Livre n'6, Editions Farel, 2001, pages 21-22)

➢ **Waɗannan matakai za su taimake ka/ki ka inganta shirin bayarwa koyaushe:**

1) Ra'ayi.

   Bayan addu'a da tunani, ɗauki ra'ayin yawan abin da kake/kike so ka/ki ba Ubangiji. Ka/ki auna menene kayayyakin da kake/kike da su kuma kana/kina so ka/ki bayar: Kuɗi, da hatsi, da lokaci, da batsira etc.

2) Ware sashe na Ubangiji

   Sa'ad da ka/kin karɓa kuɗi ko kayayyaki, ware a gefe nan da nan sashe wanda ka/kin yi niyya na Ubangiji. Waɗannan kayayyaki na Ubangiji bai kamata ka/ki yi amfani da su domin bukatunka/ki ba.

3) Rarrabawa

   Rabuwar waɗannan kayayyaki bisa jagora ka/ki karɓa ta wurin addu'a. Yana da kyau a ba da kyautai koyaushe. Ka/ki tabbatar ka/kin ba da fifiko ga Ikkilisiyarka/ki na masu bi. (Dubi zāne a ƙasa).

4) Kara kyautai da ƙara yawan abin da kake/kike bayarwa a hankali yayin da Ubangiji ya sa ka/kin bunƙasa.

➢ **Domin ka auna ga wanene za ka/ki bayar, cika wannan wurarren da aka zāna:**

| Ga wanene ko<br>Ga wane hidima? | Nawa ne? | Sau nawa? | Don me? |
|---|---|---|---|
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |

➢ **Wanda ya ba da amanar kuɗinsa ga Allah ya miƙa kansa ga Allah.**

## Karin Bayani G: A yi Shirin kadaici da Allah kowace rana

- Kasa shi ne jerin ayyoyin da aka shirya domin sadarwa tare da koyarwa na kowane darasi. Waɗannan ayyoyi za a yi amfani da su kowane lokacin da za a yi bincike da nazarin Kalmar Allah domin inganta ganewarka/ki na kowane darasi.

### *Darasi 1- Ruhu Mai Tsarki/mako 1:*

Rana 1 **Yohanna 14;15-18, 25-27**

Rana 2 **A.M. 1;4-8, 2:1-4**

Rana 3 **Yohanna 7:37-40**

Rana 4 **Zabura 139:1-10**

Rana 5 **Romawa 8:26-27**

Rana 6 **Romawa 5:1-5**

### *Darasi 2- Kalmar Alla/mako 2:*

- Kowace rana yi amfani da hanyar binciken Littafi Mai Tsarki daga **Karin Bayani B** a bisa ka/ki yi binciken, da nazari a kan ayyoyin da suke ƙasa.

Rana 1 **Zabura 119:105**

Rana 2 **Zabura 1:1-3**

Rana 3 **Matiyu 7:24-27**

Rana 4 **A.M. 17:10-14**

Rana 5 **Matiyu 8:23-27**

Rana 6 **Bitrus 1:16-21**

### *Darasi 3- Addu'a/mako 3:*

- Kowace rana, ana wayar da ayyukan addu'a daga **Karin Bayani D** a bisa.

Rana 1 **Yabo da sujada** – Zabura 100

Rana 2 **Nazari** – Joshuwa 1:8-9

Rana 3 **Furtawa**– Zabura 32

Rana 4 **Jiran Ubangiji** – Makoki 3:22-26

Rana 5 **Adduár godo** – Yakub 5:14-18

Rana 6 **Roƙo** – Filibbiyawa 4:6-7

### *Darasu 4 – Azumi da Nazari/mako 4:*

- Yi nazari kowace rana a kan shafin Nassi a cikin bincikenka/ki da lokacin sujada. Kan maganar nazari an bayar kowane da ayya.
- Zaɓa rana ɗaya domin a ɗauki lokacin azumi domin wata damuwa mai tsananni.

Rana 1 Nazari a kan **Zabura 25** – Menene albarkun neman Allah?

Rana 2 Nazari a kan **Matiyu 11:28-30** – Yi addu'a ta wurin amfani da waɗannan ayyoyi sa'an nan ka jira Allah ka tambaye shi yă nuna inda za ka ɗanɗana hutunsa.

Rana 3 Nazari a kan **Zabura 19** – Yayane Kalmar Allah ta fi zuma zaƙi a gare ka?

Rana 4 Nazari a kan **Ishaya 58:1-12** – Menene azumi na gaskiya?

Rana 5 Nazari a kan **Zabura 131** – Menene jin daɗin yaron da aka bari renonsa yakan karɓa daga zama a kan cinyar mamarsa?

Rana 6 Nazari a kan **Karin Magana 2** – wadanne amfani ne ana samu ta wurin neman hikima?

### *Darasi 5 – Ikkilisiya/mako 5:*

- Yi nazari kowace rana a kan shafin Nassi a cikin bincikenka/kenki da lokacin sujada. Kan magana an riga an bayar da kowace ayya.

Rana 1 **Zabura 84** – Marmarin yiwa Allah sujada a cikin haikalinsa

Rana 2 **Zabura 133** – Farin cikin zumunta tare da mutanen Allah

Rana 3 **Malakai 3:8-12** – Muhimmancin girmama Allah da baye-bayen mu

Rana 4 **Ibraniyawa 10:19-25** – Motsa juna zuwa ga ƙauna da ayyukan kirki

Rana 5 **2 Korintiyawa 8:1-5** – Gurbin bayarwa hannu sake a cikin Ikkilisiyar Makedoniya

Rana 6 **Kolossiyawa 3:12-17** – Karfafa juna a cikin jiki

**Karin Bayani H: Menene za ka/ki yi sa’ad da Allah ya yi kamar yayi nisa?)**

- An saba, sa’ad da muka ɗauki lokaci domin saduwa da Allah, mukan cika da tabbacin kasancewarsa da lada tare da salama da farin ciki. Amma wani lokaci duk da nemansa cikin aminci yakan zama kamar ba ya nan. (Dubi Zabura 77)
- Menene za mu yi? Ga waɗansu tunani da ra’ayoyin da za su iya taimaka:

    - **Tunawa.**

      Tuna baya a kan yadda Allah ya albarkace ka kwanan nan ka gode masa dominsa. Tuna da ayyukansa masu girma a dā. Alkawaransa da halayansa ka/kin yabe shi (Zabura 77:10-15). Nan da nan zai tarar kana/kina da dalilan da za ka/ki yi farin ciki.

    - **Maimaita.**

      Karanta Nassi ko yabo da waƙa. da babbar murya Koyaushe abokan gāban ruhaniya suna kawo mana yaƙi, sukan gudu, sa’ad da sun gane harin su yana ƙara yabon Ubangiji ne.

    - **Sake duba.**

      Auna zuciyarka domin ka tabbatar babu wani zunubin da ka yi banza da shi domin kawar. Idan so shi ne samu, furta ka kuma roƙi Allah yă sāke cika ka sabo da Ruhunsa.

    - **Kwashe mutane.**

      Tattara ’yan’uwa maza da mata domin yaƙi da su cikin addu’a.

    - **Ganewa.**

      Allah yakan yi amfani da lokacin bushewar ruhaniya yă ƙara bangaskiyarmu. (Waɗansu sun kira wannan ‘lokacin duhun rai’.) Muna girmama Allah ba kaɗan ba, yadda Ayuba ya yi, lokacin da mu manne gare shi, muna jira sai ya biya mana bukata sabo.

✧